




Musa yana da Zomo.
Musa yana ƙaunar zomon.
Ya gina wa zomo gida.
Yana ba zomo ciyawa
isasshiya.




Kowace safiya Musa na ba
zomo ciyawa.
Amma zomo ba ya godiya.




Akwai daji a bayan gidan zomo.
Dajin akwai ciyawa da yawa.
Ciyawar na da kyau a ido.


Wata rana Musa ya kawo wa
zomo ciyawa.
Zomo ya ƙi cin ciyawa.
Idon zomo na kan ciyawar
daji.




Sai zomo ya fara neman
hanyar fita.
Zomo yana son ya ci ciyawar
daji.



Zomo ya fara tona rami.
Zomo yana tono da safiya.
Zomo yana tono da rana.
Zomo yana tono da dare.



Zomo ya samu ya fita.
Ga ciyawa mai kyau a daji.
Zomo yana marmarin ciyawa.
Ya nufi dajin a guje.



Kwatsam.
Zomo ya faɗa a cikin ruwa.
Ashe ba daji bane.
Ashe fadama ce.
Karshen zomo ke nan.